
# MAGAMA

Maris 2006 Safar/Rabiul-Awwal 1427 Kyauta



## Yaƙi da Yaɗuwar Masassarar Tsuntsaye Na Bukatan Haɗin Gwiwa

ISSN 0794-0262

# Bikin Tunawa Da Samun 'Yancin Amirka A Abuja Da Legas



Ambasada John Campbell da Muƙaddashinsa, Mista Thomas P. Furey ne suke gaisawa da manyan baƙi.



Ambasada John Campbell na gaisawa da Shugaban Majalisar Dattijai, Cif Ken Nnamani.



Ambasada John Campbell na marhabin da isowar Malama Jamila Farris tare da Mista Howard Sullivan.



Gwamnan Jihar Kuros Riba tare da Uwargidansa sun halarci biki da aka shirya a ƙaramin ofishin Jakadancin Amirka da ke Legas.



Kanal Sue Ann Sandusky ce take zantawa da Shugaban Rundunonnin Sojojin ƙasa na Nijeriya, Janar Martins Agwai.



Jami'ar Sashen Al'adu, Mis Bene Uche ce take gabatar da Farfesa Ralph Akinfeleye na Jami'ar Legas ga Ambasada John Campbell da kuma Mista Brian Browne, Babban Wakilin Amirka a ƙaramin ofishin Jakadancinta da ke Legas.

# MAGAMA

Maris 2006 Safar/Rabiul-Awwal 1427 Kundi Na 1, Fitowa Ta 22




Kwanan nan Ofishin Jakadancin Amirka a Nijeriya ya kammala dukan harkokin da ya shirya yi a bana. Don haka sakamakon da muka samu ba zai zama abin mamaki ga jama'ar Nijeriya ba. Gwamnatin Amirka ta haƙiƙance a kan tabbatar da haɗin kai tsakanin jami'ai da jama'ar da abin ya shafa, domin ƙarfafa harkokin ɓangarorin mulkin dimokuraɗiyya da dakushe yaɗuwar cutar ƙanjamau da sauran munanan cututtuka da inganta harkokin bunƙasa tattalin arzikin ƙasa da magance tashe-tashen hankula da ayyukan ƙungiyoyin ta'addanci da aikata laifuka, a yankin. Wannan niyyar ma kaɗai, abin alfahari ce. Ina kuma faɗa da babbar murya cewa, mun samu gagarumar nasarar haɗin kai, ba kaɗan ba.

A wannan fitowar, mun mayar da hankalinmu ne ga irin gagarumin haɗin gwiwar da ke tsakanin jama'ar Nijeriya da sauran ƙasashen duniya. Cikinsu kuwa har da yunƙurin ƙasashen Amirka wajen ƙalubalantar masassarar tsuntsaye. Bugu da ƙari domin bayar da cikakkun bayanai da gaskiyar al'amari game da cutar masassarar tsuntsaye, wanda ya nuna a zahiri, irin hanyoyin da suka kamaci a bi, wajen rigakafin yaɗuwar cutar ta masassarar tsuntsaye. Mun kuma yi cikakken bayani game da dukan irin tambayoyin da za a yi, game da cutar ta masassarar tsuntsaye, a lokacin da annobar cutar ta so ta yi ƙamari.

Ambasada John Campbell ma ya yi bayani game da muhimmancin matasa, a matsayin ginshiƙin harkokin ci gaban ƙasa, a wani ƙasaitaccen jawabin da ya yi a Jami'ar Obafemi Awolowo da ke Ile-Ife, inda ya ƙalubalanci matasan Nijeriya "da yin koyi da yadda duniya ke tafiya, su kuma binciko hanyoyin da kan iya kawo canji".

Al'amarin babu kama hannun yaro. Kada a shagala da rahoton Sani Mohammed a kan tarihin baƙar fatar Amirka, da kuma bikin da suka yi, domin tunawa da muhimmancin rayuwarsu. Wannan fitowar ta kuma kawo muhimman labarai game da rubuce-rubucen da James Moolom da Susan Jatau suka yi, game da Taron Bikin Tunawa da Shekaru Shida da Kafuwar Kungiyar Ɗaliban Shirin Fulbright Na Nijeriya da aka yi a Kano.

Kamar yadda za ku gani a shafuffukan, Ofishin Jakadancin Amirka na taimaka wa 'yan Nijeriya da kansu, wajen warware matsaloli da ƙara ƙwarin gwiwa da fuskantar duk wata ƙalubalar rayuwa, kazalika da haɗa ƙarfi waje guda, don tanadin abincin da Nijeriya ke nomawa.

*Atim Eneida George*

## Abubuwan Da Ke Ciki


Kwararru Daga Amirka Su Na Taimaka Wa Nijeriya Yaƙar Ɓarkewar Cutar Masassaran Tsuntsaye — 2

Amirka Ta Bai Wa Nijeriya Kayayyakin Yaƙi Da Annobar Cutar Masassaran Tsuntsaye — 3

Shawara Ga Jama'ar Da Ke Zaune A Yankuna — 4

Cigaban Bayyani Game Da Allurar Rigakafin Shan-Inna — 7

Taimakon Gaggawa Na Shugaban Amirka A Kan Kanjamau — 8

An Yi Bikin Tunawa Da Samun 'Yancin Amirka Bikin Tunawa Da Tarihin Baƙar Fatar Amirka — 10

Taron Shekara Na Shida Na Tsofaffin Ɗaliban Shirin Fulbright A Nijeriya Ya Tattauna Hanyoyin — 11



MA'AIKATAN MUJALLA

CLAUDIA E. ANYASO
Jami'ar Hulɗa Da Jama'a A Nijeriya

RUDOLPH E. STEWART
Jam'in Labarai

SANI MOHAMMED
Edita

ISHAKA ALIYU
Mai Ba Da Shawara Game Da Wallafawa



Ofishin Jakadancin Amirka ke wallafa wannan mujallar kowane wata. A aiko da wasiƙu zuwa ga
Sashen Hulɗa da Jama'a, Lamba 1075 Titin Difulomasiyya, Tsakiyyar Gari, akwatin gidan waya mai lamba: 5760, Abuja, Nijeriya.
09-4614000 Fax: 09-4614011. Ofishin na Legas: akwatin gidan waya mai lamba: 554, Legas.
Tel: 01-2632577, 2633560, 2633395. Na'urar INTERNET: http://nigeria.usembassy.gov/wwwhmagama.html

# Nijeriya Ta Duƙufa Kan Dakushe Yaɗuwar Cutar Masassarar Tsuntsaye




*Kwamitin ƙwararru da Shugaba Obasanjo ya naɗa domin magance yaɗuwar cutar masassarar tsuntsaye.*

Daga
*Idika U. Onyukwu tare da Sani Mohammed*

Aranar bakwai ga watan Fabrairun bana ne Kungiyar Abinci da Aikin Gona ta Majalisar Ɗinkin Duniya ta ba da tabbacinsa a kan ɓullar cutar masassarar tsuntsaye mai ɗauke da ƙwayar HPAI H5NI a cikin kajin da ke gonar kiwon kaji ta Sambawa da ke jihar Kaduna a arewacin Nijeriya. Ya zuwa ranar 22 ga watan Fabrairu, babu wani labarin wani ɗan Adam da ya kamu da wannan cutar. Bayan haka, an samu



© AP

*Wani gonan kaji da wannan annobar cutar masassarar tsuntsaye n ya shafa a Kano.*



Wani kasuwan kaji a arewacin Nijeriya..

© AP



Wannan mutumin na kokarin binne kajinsa da suka mutu a dalillin wannan annobar masassaran tsunstaye.

labarin ɓullar wannan cutar ta H5NI a wasu gonaki a jihohi 11 da ke cikin ƙasar n an.

Bayanin wasu ƙwararru haɗe da Dr. David Henzler na Sashen Harkokin Gona na ƙasar Amirka da ke Pennsylvania da kuma Dr. Jan Michaux na Hukumar Kula da yaɗuwar cututtuka a ƙasashen Kungiyar Tarayyar Turai (PACE) sun ce, ƙila ɓullar wannan cutar massasarar tsuntsayen ta abku cikin makonni da dama kafin a gano wannan ƙwayar H5NI, a cikin jihar Kano. Kaji da dama sun mutu daga cututtuka da ba san su ba a cikin watan da ya biyo baya, wanda ya sa aka ɗauki matakin gwaje-gwaje. Makiwatan kaji da dama sun sayar da kajinsu cikin gaggawa bayan samun labarin ɓullar wannan ƙwayar ta H5NI, domin su rage hasara

MATAKI DAGA NIJERIYA

Ya zuwa yanzu, Gwamnatin Tarrayar Nijeriya ta ɗauki matakin gaggawa domin keɓe gonakin da wannan annobar ta shafa, da kuma karkashe kajin da suka kamu da cutar ta massasarar tsuntsaye mai ƙwayar H5NI da waɗanda suke nuna halamar kamuwa da cutar amma ba a tabbatar da hakan ba. A Dalilin hakan, Ministan Ma'aikatar Labarai da Wayar da kan Jama'a, Mista Frank Nweke, Jr ya ba da sanarwa cewa a kashe duk kajin da ake kiwo a tsakannin kilomita 3 daga inda aka samu ɓullar wannan cutar. Hukuma ta ɗauki wannan mataki ne, kafin ma, a fito da hanyoyin biyan diya ga waɗanda suka rasa dukiyoyyinsu ga wannan annobar. Hakan ya sa Kungiyar Gonakin Kiwon Kaji ta ƙasa suka koka cewa kuɗaɗe da aka kiyasta za a biya su akan ko wane kaji ko tsuntsu da aka kashe sunyi kaɗan. Maƙi yawan lokaci abinda aka biya masu kiwon tsuntsayen bai wuce tsakanin Naira 250 zuwa Naira 1000 a wasu sassa na Nijeriya.

A yanzu haka, hukumomin kiwon lafiya na haɗin gwiwa na ƙoƙarin gwada ma'aikatan gonakin kiwon tsuntsayen domin tabattar da ko sun kamu da cutar ta H5NI. Gwamnatin Nijeriya ta nemi taimako daga ƙungiyoyi da ƙasashen waje domin samun ƙwaƙƙwarar hanyar magance yaɗuwar wannan bala'i ta annobar H5NI.

GUDUNMAWAR AMIRKA DA SAURAN KASASHEN DUNIYA

Jim kaɗan da bayyana sakamakon ɓullar annobar Masassaran Tsuntsaye (watau Murar Kaji), a wata gonar da ke Arewacin Nijeriya, ranar 8 ga watan Fabrairu, sai Gwamnatin Amirka ta bayyana bayar da gudunmawar dalar Amirka miliyan

# Gudunmawar Amirka Da Sauran Kasashen Duniya



*Muƙaddashin Jakadan Amirka a Nijeriya, Mista Thomas P. Furey, a lokacin da yake miƙa kayayyakin kariyar ma'aikatan da ke yaƙar wannan annobar ga Ministan Ma'aikatar Aikin Gona, Alhaji Adamu Bello.*



© AP

*Jami'an Ma'aikatan gona sanye da kayan karesu daga kamuwa da H5N1.*

25 ga Nijeriya, kazalika da kyautar kayayyakin aikin yaƙar annobar har dubu biyu, don taimakawa ga irin yunƙurin da ake yi na dakushe yaɗuwarta. Ranar Talata 14 ga watan Fabrairu ne Muƙaddashin Jakadan Amirka, Mr. Thomas P. Furey, ya gabatar da irin kayayyakin da aka bayar kyauta ga Ministan Aikin Gona, Alhaji Adamu Bello. Minista Bello ya ce irin hanzarta bayar da gudunmawar da Amirka ta yi, da kuma cika alkawarin da ta yi, ya nuna irin dangantakar da ke tsakanin Amirka da Nijeriya, wajen magance annobar ta cutar masassaran tsuntsayen. Kuma tallafin na Amirka, haɗe da bayanan yadda za a shawo kan al'amarin annobar tsuntsayen, ya sa Ministan Aikin Gona, Alhaji Adamu Bello, ya kafa Kwamitin Wayar da Kan Jama'a, don ba shi shawarwarin gaggawa na yadda za a yi, a cikin awowi 24.

Shugaba Olusegun Obasanjo kuma ya ƙara wa Barno dawaki, inda ya kira taron dukan ƙungiyoyin duniya, mazauna Nijeriya, da ke bayar da taimako, don gode masu game da hanzarta bayar da tallafin da kuma taimako.

Har ila yau, Gwamnatin Tarayyar Nijeriya ta bayyana kafa Cibiyar Kula da Matsaloli a Babbar Fadar Gwamnati da ke Dutsen Aso, domin su karɓa da tattara bayanai da wayar da kan jama'a dangane da yadda za a shawo kan annobar masassarar tsuntsayen. Ministan Aikin Gona da na Kiwon Lafiya da kuma wakilan Hukumar Kiwon Lafiya ta Duniya (WHO) da Hukumar Noma da Abinci ta Duniya (FAO) da Kungiyar Kasashen Turai (EU) da Hukumar Raya Kasashe Waje ta Amirka (USAID), su ne ke cikin wannan kwamitin. Gwamnatin Tarayyar Nijeriya kuma ta naɗa ƙananan kwamitocin harkokin fasaha da sadarwa.

Kwamitin Fasahar yana ƙarƙashin shugabancin Karamin Ministan Aikin Gona, Cif Bamidele Dada, yayin da Kwamitin Sadarwa ke ƙarƙashin Ministan Labarai da Wayar da Kan Jama'a, Mr. Frank Nweke Jnr.

Gwamnatin Tarayya ta yi kira ga jama'a da kada su firgita "domin ana yin duk abin da ya kamata don shawo kan ɓullar cutar".

Gwamnatin ta tabbatar wa masu kiwon kaji cewa duk wanda aka kashe wa tsuntsaye, to za a biya shi diyya. Matakan gaggawa na kwanaki 120 da USAID ta gabatar domin taimaka wa Nijeriya dakushe wannan annobar sun haɗa da karkashe tsuntsayen da suka kamu da wannan cutar, da yaɗa hanyoyin hana yaɗuwar cutar da kuma taimakon

# Shawara Ga Jama'ar Da Ke Zaune A Yankunan Da Annobar Cutar Masassaran Tsuntsaye Ta Ɓulla

## *Babbar Shawara Da Saƙonni*

Ana iya yin rigakafin yaɗuwar cutar Masassaran Tsuntsaye a wuraren da ta ɓulla

❖ Jama'a su ƙaurace wa cuɗanya da kaji da agwagi ko sauran tsuntsaye, sai idan ya zama dole. Wannan ita ce hanya mafi a'ala ta yin rigakafin kamuwa da cutar masassarar tsuntsaye.

❖ Kananan yara sun fi kamuwa da cutar domin su ke yin wasanni a inda ake kiwon tsuntsayen. Koya wa yaranka waɗannan dabarun:

- Kaurace wa cuɗanya da tsuntsaye, ko gashinsu, ko kashinsu ko kuma sharar wurin.
- Kada a ajiye tsuntsaye don yin wasanni.
- A wanke hannuwa da sabulu da ruwa bayan an taɓa tsuntsayen.
- Kada a kwanta kusa da inda ake makiwatan tsuntsayen ta hanyoyin farfaɗo da sana'o'insu. Hanyoyi mafi ɗorewa kuma su ne, na ba da taimakon ƙwararrun likitocin kiwon lafiyar tsuntsaye da na aikin gona da na dabarun kiwon tsuntsaye da kuma masu ba da shawara kan hanyoyin farfaɗo da harkokin cinikin tsuntsaye. Har ila yau, akwai taimakon haɗin gwiwa da Cibiyar Bincike da Rigakafin Cututtuka ta Amirka (CDC) da Hukumar Abinci da Noma ta Duniya da Kungiyar Lafiyar Dabbobi (OIE) da kuma Kungiyar Kiwon Lafiya ta Duniya (WHO) suke yi.



Wannan yaro da ba ambaci sunansa ba, ya kamo wata 'yar kaza. To hatara dai yaro, domin a wannan hali da ake ciki, kaza ba abokiyar wasa ba ce.

KOKARI A MAKWABTA

Kasar Nijar da ke maƙwabtaka da Nijeriya ta arewa ta bada labarin ɓullar kwayar cutar H5NI na masassarar tsuntsaye a ƙasar. Haka kuma maƙwabciyar Nijeriya ta yamma, watau ƙasar Kamaru ita ma, ta ba da sanarwar ɓullar wannan cuta a ƙasarta. A cikin watan Janairun bana ne, Hukumar Abinci da Noma ta Duniya ta yi taronta na 24 a yankin Afirka a ƙasar Mali domin tattauna hanyoyin magance cutar masassarar tsuntsaye a yankunan Afirka. Kasashe 18 ne suka halarci wannan taro, a inda aka bayyana cewa ƙasashen yankin Afirka huɗu ne kawai suke da ɗakuna da ingantattun na'urorin binciken kwayar H5NI, amma kuma akwai isassun kwararrun waɗanda ke iya yin wannan aikin ma'aikatan binciken a yankin.

A cikin watan Oktobar bara, Kungiyar Kiwon Lafiya ta Duniya (WHO) ta ƙiyasta cewa ƙasashen Afirka na cikin hasara kwarai, kuma akwai yiwuwar mutane su kamu da wannan cutar, da zaran ta shiga jikin mutum, tana iya canza yanayi ta kuma yaɗu nan-da-nan domin yawan cuɗanya da mutanen yankin ke yi da tsuntsaye a ko da yaushe. Kungiyar ta ƙalubalanci shirin da ƙasashen yankin na Afirka ke da su na hana kamuwa da kwayar na H5NI wadda ke iya zama babbar matsala ga yaɗuwar wannan cuta a sauran ƙasashen duniya. ■

kiwon tsuntsaye.

• A guji ɗaukar kaji ko agwagi matattu ko masu rai daga wani wuri zuwa wani wuri, ko da kuwa an san cewa suna da lafiya.

❖ Kada a bari a canja wa tsuntsayen da suka kamu da cutar wuri.

❖ Kada kuma a bai wa jama'a ko dabbobi naman tsuntsayen da suka kamu da wannan cutar. Yankasu da cinsu babban haɗari ne.

❖ Idan har aka yi cuɗanya da kashi, ko gashi, ko ruwan sha da abinci, ko wurin kiwon irin waɗannan tsuntsayen, bisa kuskure, to a yi ƙoƙarin:

• Wanke hannu da ruwa da sabulu, a duk lokacin da aka taɓa.

• Cire takalma kafin a shiga gida, a kuma wanke dukan datti; da

• Duba yanayin lafiyar jiki, a kowace rana idan zafin jiki ya hau ya zuwa fiye da 37.5, to a hanzarta zuwa wurin likita ko asibiti mafi kusa domin duba lafiya.

Sanin yadda za a yi cuɗanya da tsuntsayen da suka kamu da cutar ta Masassaran Tsuntsaye yana da muhimmanci, domin rigakafin yaɗuwarta.

❖ A tabbatar da hana yara kusantar matattu ko tsuntsayen da suka kamu da cutar.

❖ Idan har dole sai an yi cuɗanya da irin waɗannan tsuntsaye, to a tabbatar da an sanya waɗansu kayayyakin kare jiki, kamar su tabarau ko takalma da safar roba. Idan babu irin waɗannan kayayyakin aikin, to a rufe bakuna da hanci da ƙyalle, a sanya tabarau da kuma yin safar hannu da ƙafa da leda, tun daga idon ƙafa har gwiwa da kuma wuyan hannu har zuwa gwiwar hannu. A kuma sanya doguwar rigar da za a iya wankewa, ta rufe ka rif.

❖ Idan aka yi arangama da



© AP

matattun tsuntsaye, ko waɗanda suka kamu, to a sanar da hukuma da wuri, a kuma bari masana yadda ake ɗawainiya da irin waɗannan tsuntsayen su gudanar da aikinsu.

Fesa magani a wuraren kiwo, ko kiwon kajin zai taimaka ga hana yaɗuwar wannan cutar.

❖ Idan zai yiwu, a tambayi masanin harkokin kiwon lafiya yadda ake feshin wurin kiwon, da inda ake kiwon kaji.

❖ Idan hakan ta gagara, dole sai kai za ka yi, to ka sanya abubuwan da za su kare idanunka da hannuwanka da ƙafafuwanka da dukan inda jikinka zai fito waje.

❖ Ya kamata a bizne dukan tsuntsayen da suka mutu (kamar yadda aka yi bayani)

❖ A tsabtace wuri tsab, kada a bar ko da gashi, ko kuma wani datti, ko najasa, a wurin kiwon.

❖ Kwayar cutar Masassaran Tsuntsaye tana daɗewa kafin ta mutu, musamman a cikin ƙazanta, don haka dole a yi amfani da sabulu wajen wanke ƙazantar. Dole kuma a cire duk wani dattin da ke wurin kiwon tsuntsayen.

❖ Tun da yake ba a iya tsabtace dukan inda tsuntsayen ke zuwa yawo, to kada a bar sauran tsuntsayen su shiga wuraren har na tsawon kwanaki 42, domin duk wata ƙwayar cutar da ke wurin ta mutu. Idan kuma lokacin hunturu ne, a ƙara yawan kwanakin.

❖ Feshin wurin da itatuwan da ke wurin yana da alfanun gaske, don ganin maganin ya shiga ƙwayoyin cutar sosai. Amma ba dole ba ne, a kankare ƙasar da ke wurin, sai dai idan ta caɓe. A rufe dukan tsuntsayen da suka mutu da kashinsu.


❖ Duk yadda za a yi, a nemi shawarar jami'an aikin gona game da yadda za a bizne irin waɗannan matattun tsuntsayen.

❖ Idan ana bizne su kuma, kada a tayar da ƙura. A riƙa yi ana yayyafa ruwa a wurin don maganin tashin ƙura. ■


# Hanyoyi Shida Na Kauce Wa Kamuwa Da Cutar Masassaran Tsuntsaye





Kada ka bari yara su kusanci wurin kiwon kaji da sauran tsuntsaye.





Bayar da rahoton mataccen tsuntsu ga hukuma mafi kusa.





Ka nemi magani da zarar ka kamu da wata rashin lafiya, bayan ka taɓa mataccen tsuntsu ko mara lafiya.




Bayar da maganin ƙwayar cutar masassaran tsuntsaye, kyauta ne.




Sabulu na kashe ƙwayoyin cuta, don haka wanke hannuwanka da ruwa da sabulu, ko yaushe.




A dafa ƙwai da kaji sosai, kafin a ci.

# ... Cigaban Bayyani Game Da Allurar Rigakafin Shan-Inna



*Allurar rigakafin Shan-inna (OPV)*

Kungiyar Malaman Islama na Duniya ta samu wata sanarwar cewa waɗansu mutane a ƙasashen Musulmi suna ƙyamar a yi wa yaransu allurar rigakafin kamuwa da cutar shan inna. Cewa akwai allurar da dama don kare yaransu daga kamuwa da munanan cututtuka da ke kashewa ko wata mummunar naƙasa. Amma bai wa yaro wannan allurar tabbaci ne ga wata dokar addini ta Annabin Tsira, wanda a cikin wani hadisi da Abu Hurayrah ya ruwaito, inda yake cewa Annabin Rahama ya ce "Duk wanda ya kare kansa daga wata masifa, to zai kuɓuta daga masifar".

Shekaru da dama, masana harkokin magunguna, a ko'ina cikin duniya, bakinsu ɗaya ne cewa allurar rigakafi na da muhimmancin gaske wajen kare mutane, musamman yara daga cututtuka da dama. Hakika, ta hanyar allurar rigakafi da kuma taimakon Allah, mutane da dama suke lafiyayyu, ba su da waɗannan cututtukan. Wannan kuma shi ya sa Kungiyar Lafiya ta Duniya da sauran ƙasashen da ke wakilcinta suka ɓullo da shirye-shirye, don kawar da waɗansu cututtuka. Fiye da shekaru 20 da suka wuce aka kawar da cutar agana daga doron duniya. Kawar da ita kuma ya taimaka wa duniya da ta yi hanƙoron kawar da cutar shan inna, wadda ke gallaza wa rayukan yara azaba. An fito da al'amuran wayar da kan jama'a da kuma bai wa yara allurar da ke da ƙwayoyin cutar shan inna matattu ko kuma waɗanda aka kassara. Ana ɗiga wa yaran ne, ko a yi masu allurarta. Duk kuma hanyar da aka bi ta tabbatar da rashin lahaninta da kuma aikin da take yi. Koƙarin da duniya ke yi na kawar da cutar shan inna ya rage yawan ɓullar cutar a duniya, daga mutane dubu da ke mutuwa a kullum ya zuwa ƙasa da dubu da ke mutuwa a shekara. Wannan ya nuna cewa ƙasashe 52 daga cikin 57 na Kungiyar Musulmi ta Duniya sun kuɓuta daga cutar shan inna.

Ko da yake wannan cutar ta ɓata daga mafi yawan ƙasashen duniya, abin takaici akwai ta a ƙasashen Musulmi biyar, da kuma wata ƙasar da ke da Musulmi 'yan ƙalilan. Wannan ya nuna ke nan, kusan yaran Musulmi ne ke ci gaba da abkawa cikin haɗarin wannan cuta, kuma ya nuna ke nan Musulmi ne ke da laifin dakushe ci gaban da ake samu na ƙoƙarin kawar da cutar shan inna a duniya.

Saboda wannan al'amarin ne, Kungiyar Musulmi ta Duniya ta yanke shawarar wani ƙuduri a 2003, inda ta kira dukan ƙasashen Musulmi da su ƙara bayar da himma don tabbatar da kawar da cutar shan inna, gaba ɗaya.

Matsala guda ita ce, irin shaihannan waɗansu ƙasashen Musulmi da ke ƙorafi a kan yin amfani da allurar rigakafin, inda suke bayar da gurguwar hujja da gardandami. Ga misali, an yi zargin cewa, allurar tana da waɗansu magunguna da abubuwan hana ɗaukar ciki, da ke da illa, kamar ta rashin haihuwa. Waɗansu kuma sun bayyana cewa tana da datti da kazantar da aka haramta sha. Suna mafarkin cewa duk abin da ake yin allurar da shi gaskiya ne. Wata faɗar ma cewa ta yi, wata kazanta ta gurɓata allurar lokacin da aka ajiye ta, ta tsima, inda har aka gano wani dallaki-dallakin dusar da aka kwaɓa da kitsen alade, duk da yake an tace ta sarai, babu wani abin da ya yi

# Taimakon Gaggawa Na Shugaban Amirka A Kan Kanjamau Ya Canja Halin Rayuwa A Nijeriya

An bayyana wa 'yan jaridu cewa, yanzu Nijeriya na cikin ƙasashe biyar da suka fi fama da cutar ƙanjamau a duniya.

An bayyana hakan ne a wajen wani taron manema labarai na kwanan nan, da Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka ya gudanar, don bayyana aikin da Cibiyar Binciken Cututtuka ta Harvard APIN (CDC) tare da haɗin gwiwar Shirin Shugaban Amirka na Tallafa wa masu cutar ƙanjamau PEPFAR ke yi.

Babban Jami'in cibiyar, Dokta Ernest Ekong, ya ce a ƙasa mai yawan jama'a fiye da miliyan 120, wadda kashi 5 cikin 100 na jama'arta ke ɗauke da cutar ƙanjamau, Nijeriya ke nan na da yawan kashi 10 cikin 100 na masu cutar a duniya.



Dr. Earnest Ekong (na farko daga hagu) tare da Mista John Vertefeuille, Daraktan CDC da kuma Babbar Jami'ar Bincike ta Cibiyar Harvard-APIN, Farfesa Phyllis Kanki (a dama).

Cibiyoyin na Harvard APIN na ƙoƙarin bayar da magani ga marasa lafiya dubu 12 da kuma waɗansu dubu 16 da 800 da ke da cututtukan da ke da nasaba da cutar ƙanjamau.

Ana kuma bai wa mata masu juna biyu shawarwari da magani na rage yawan waɗanda ke harbin jariransu da cutar.

A bisa ga horon da ake bai wa ma'aikata, yanzu Cibiyar ta Harvard ta buɗe wuraren shan magani 25 a Nijeriya, inda cibiyar ke tallafa wa marasa lafiya dubu 12 a ƙarƙashin Shirin Bayar da Maganin da ke inganta garkuwan jikin wanda ya kamu da cutar Kanjamau (ART) ta ƙasa.

Daraktan Yanki na Cibiyar CDC, John Vertefeuille da Babban Jami'ar Bincike na Cibiyar Harvard APIN, Farfesa Phyllis Kanki, sun halarci taron 'yan jaridun. ■

---

kama da dusa. Hasali ma, wani tsabtatacen ruwa ne aka zuba, don a riƙa bai wa kowane yaro ɗigo ɗaya ko biyu.

Kungiyar Musulmin Duniya tana son ta tabbatar da cewa:

1. Haƙƙin kowane Musulmi ne ya guje wa haɗari, ta kowane fanni, domin kada su kai kansu cikin halaka, ko shiga cikin wani mawuyacin halin da zai hallaka su. Rai dai wata amana ce da Allah ya bai wa mutum, kuma ya haramta a jefa shi cikin haɗari. Allah a cikin AlKur'ani ya bayar da umurnin cewa: "Kada ku jefa kawunanku cikin halaka da hannayenku" (2:195). "Kada ku kashe kawunanku, Allah mai Rahama ne a kanku" (4:29). A nan muna iya kawo misali da Amr ibn al-Aas, wani sahabin Annabin Rahama da aka tura zuwa wurin yaƙi. Da ya samu kansa cikin janaba, a wani dare na hunturu, duk da haka sai ya jagoranci yin sallah, ba tare da ya yi wanka ba. A nan sai ya yi taimama. Waɗanda ke tare da shi, a wajen yaƙin, sai suka fara wasi-wasin abin da ya aikata, suka kai ƙara ga Annabin Rahama. Sai ya bayyana cewa "Ya Manzon Allah! Daren yana da matsanancin sanyi, na kuma tuna Ubangiji ya ce, "Kada ku kashe kawunanku, Allah mai Rahama ne a kanku". Sai Annabin Rahama ya yi murmushin tabbatar da abin da ya faɗa na fahimta. Wannan misalin ne na dokar da ta tabbatar da aikata wani abu. Akwai kuma dokar Musulunci da ta ce: "A kauce wa haɗari, ta yadda za a iya". Madogarar wannan dokar wani hadisin Annabin Rahama ne da ya ce: "Kada a kuskura, a cutar da wani, ko waɗansu" (Ibn Majah da al-Daraquitni da al-Hakim suka ruwaito shi, a littafin Al-Arbaeen al-Nawawiyyyah). Wata kuma dokar irin wadda aka bayyana, ta ce, "An fi bayar da lada ga wanda ya hana cutarwa da wanda ya kawo abin amfani".

*Akwai ƙarin bayani a fitowarmu na gaba.* ■

# An Yi Bikin Tunawa Da Samun 'Yancin Amirka

Amirkawa, tare da jama'ar Nijeriya daga kowane jinsin jama'a da jami'an hulɗar jakadanci, a Nijeriya, sun taya Amirka tunawa da samun 'yancinta, ranar 25 da kuma 28 ga watan Fabrairu, a Karamin Ofishin Jakadancin Amirka da ke Legas da kuma Babban Ofishin Jakadancinta da ke Abuja.

Lokacin da yake marhabin da baƙi, Jakadan Amirka a Nijeriya, Mista John Campbell ya ce, an sake tsayar da ranar Bikin Tunawa da Amirkan ne, don kauce wa ruwan damina, daga 4 ga watan Yuli, zuwa watan na Fabrairu, don ya zo daidai da Bikin Tunawa da Shugabannin Amirka. Manyan baƙin da suka halarci bikin na Abuja da Legas sun haɗa da Babban Jojin Nijeriya, Alhaji Mohammed Uwais da Shugaban Majalisar Dattijai Ken Nnamani da gwamnonin Kaduna da Kros Riba da kuma jami'an tsaron ofisoshin jadakancin ƙasashe da dama.

Tun da farko Jakada Campbell ya yanka ket da Hukumar Gudanarwar Otel ɗin Sheraton Hotels and Towers ta yi masu, don tunawa da ranar. ■



*Sojojin Amirka da ke kare Ofishin Jakadancin Amirka a Abuja suna girmama ƙasar, a lokacin da ake buga taken Amirka a wannan biki.*



*Ambasada John Campbell ( a hagu) tare da Ambasada Sanusi Bayero (tsakiya) da ɗan Majalisar Dattijai, Senata Udo Udoma, sai kuma Alhaji Muktari Shitu na Sashen Siyasa*



*Babban Jojin Nijeriya, Alhaji Mohammed Uwais tare da manyan baƙi da suka taya Amirka murnar wannan rana ta tunawa da samun 'yancin Amirka.*



*Maigirma, Gwamna Muhammed Ahmed Maƙarfi na Jihar Kaduna, shi ma ya halarci wannan biki.*

# Bikin Tunawa Da Tarihin Baƙar Fatar Amirka

Daga Sani Mohammed,
Editan MAGAMA




*Wakiliyar Gidauniyar Leon H. Sullivan, Misis Hope Sullivan Masters (a tsakiya) tare da Misis Shirley Lisenby, Jami'ar Sashen Al'adu na Ofishin Jakadancin Amirka (hagu) da kuma wakilan wannan Gidauniya.*

Sassan Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja da Legas, sun shirya Bikin Tunawa da Tarihin Baƙar Fatar Amirka na wannan shekarar, da shagulgula a kan irin ɗimbin gudunmuwar da baƙaƙen fatar Amirka suka bayar, wajen ci gaban Amirka, musamman, da duniya baki ɗaya.

Misis Hope Sullivan-Masters ce ta fara buɗe taron a Abuja da yi wa manema labarai jawabi ranar 9 ga watan Fabrairu.

Ta yi bayanai da dama game da irin ɗimbin gudunmawar da mahaifinta, marigayi Reberan Leon Sullivan ya bayar dangane da ƙulla zumunci tsakanin jama'ar Nijeriya da Amirka. Ta kuma yi bayanai game ƙoƙarin Reberan Sullivan, na tara shugabannin duniya da manyan mawallafa harkokin zamantakewa da kuma aiwatar da waɗansu shirye-shirye nagari.

Reberan Sullivan, mutum ne jarumi, wanda ya mutu ranar 24 ga watan Afrilun 2001. An kuma kafa Gidauniyar Leon H. Sullivan a 2001, ba don girmama irin rayuwar da ya yi ba kaɗai, da ma irin yadda ya shugabanci gagarumin canjin tattalin arziki da zamantakewar baƙar fatar Amirka da taimaka wa ɗan-Adam, har ma da inganta harkokin ci-da-gumi don tallafa wa marasa galihu da bayar da shawarwarin harkokin zaman-takewa. An shirya za a sake yin taron gidauniyar na biyu, a Nijeriya, a watan Yulin 2006. Taron na farko an yi shi ne a Abuja, a 2003, inda har Shugaba George W. Bush da Shugaba Olusegun Obasanjo suka zama manyan baƙi.



*Gabatarwa daga Jami'ar Sashen Al'adu na Ofishin Jakadancin Amirka. A cikin manyan baƙi da suka halarci taron, akwai Alhaji Usman Jimada, Jami'i a Hukumar Daidaita Wakilcin Al'umma a Harkokin Gwamnati (a dama).*

Lokacin da take jawabi a wajen bikin tunawa da Tarihin na Baƙar Fatar Amirka, Jami'ar Harkokin Al'adu ta Ofishin Jakadancin, Shirley Lisenby ta ce al'amurran suna da dama, a bikin, cikinsu kuwa har da tattaunawa game da ɗawainiyar da ta rataya a wuyanmu da 'yancin da tsarin mulki ya ba mu da dokoki da mulkin dimokuraɗiyya da shugabanci nagari da kuma bunƙasa tattalin arziki.

Ɗaya daga cikin bukukuwan da Cibiyar Harkokin Fasahar Watsa Labarai ta Bola Ige ta shirya, a Cibiyar Amirka da ke Abuja, ita ce



Senata Hillman Frazier tare da Hajiya Saudatu Sani. shugabar kwamitin Harkokin Mata a majalisar Tarayya.

Daga Shafi Na 11

wata lacca a kan "Gina Tafarkin Dimokuraɗiyya ga Jaririyar Gwamnatin Dimokuraɗiyya", sai kuma tattaunawar da Ɗan Majalisar Dattijai Hillman Terone Frazier da shugabar Kwamitin Harkokin Mata na Majalisar Tarayya, Saudatu Sani, suka yi. A taron da ɗimbin jama'ar Nijeriya suka halarta, Ɗan Majalisar Dattijai Frazier, wanda yake wakilcin Yankin Hinds Country na 27, da ke Jihar Mississippi, ya bayar da shawarar a riƙa jiɓintar juna, don zama wani jigon gina tafarkin dimokuraɗiyya. Lokacin da yake bayar da misali, Ɗan Majalisar Dattijai Frazier, ya bayyana cewa, ba za a taɓa samun nasarar jiɓintar juna ba, sai an ji ta bakin kowa. "Ko taken Nijeriya da na Amirka, sai da aka kaɗa aka busa, kafin a rera su", in ji shi. Sauran bukukuwan sun shafi 'yancin ɗan-Adam da hanyoyin girmama muƙaman wakilan majalisu da shugabanci. Ya kuma tuno da irin gudunmawar da waɗansu fitattun mata a Amirka suka bayar, na shugabantar mata da ƙwato masu 'yanci, waɗanda suka riga mu gidan gaskiya kwanan nan, watau Rosa Parks da Corretta Scott King. Ya kuma yi kira ga jama'ar Nijeriya da su yi koyi da irin gwagwarmayar da baƙar fatar Amirka suka yi. Bugu da ƙari Sashen Hulɗa da Jama'ar ya karɓi baƙuncin nuna majigi a watan na Fabrairu.

Fina-finan, da aka nuna wa ma'aikatan ofishin jakadancin su ne, kamar su *Amistad, Mama Flora's Family* da kuma jawaban Martin Luther King Jr. Ita kuma cibiyar ilimi ta Ofishin Jakadancin ta nuna waɗansu fina-finai game da tarihin Dokta Martin Luther King Jr., a wani ɗan zaman da ta yi da jama'a, a Cibiyar Al'adu da Gargajiya ta Babban Birnin Tarayya, Abuja. ■

# Shirin Shige-da-Ficen Ɗalibai:

## *Yana Karfafa Tsaron Kan Iyakoki da Buɗe Kofar Sani*

Gwamnatin Amirka tana mai farin cikin bayyana cewa ta ƙara tsawon lokacin da ake bai wa ɗaliban ƙasashen waje iznin koyon karatu.

Wannan na ɗaya daga cikin ƙudurorin da Shirin Rice-Chertoff Joint Vision ya ɗauka domin inganta tsaron kan iyakokin ƙasa, da daidaita harkokin tsaro da gudanar da safarar baƙi da ke shiga Amirka.

Dukan ɗaliban da suka nemi iznin shiga Amirka masu laƙabin F-1 da F-2 da M-1 da kuma M-2, za su iya zaman kwanakin kashe wando har 120 kafin su fara karatu, idan aka kamanta da kwanaki 90 da ake bayarwa a da.

Masu neman iznin zaman kuma na rukunin J-1 da J-2 na iya samun iznin a duk lokacin da suke so kafin fara makaranta.

Waɗannan canje-canje sun shafi sababbin ɗalibai ne kaɗai. Amma tsofaffin ɗalibai sai sun sake neman iznin na rukunin F da M, kowane lokaci, muddin suna bukatar ci gaba da kasancewa ɗalibai, idan kuma dukan Bayanan Ɗalibci da Musayar Baƙi (SEVIS) a kansu bai da wata tangarɗa.

Don zama wani ɓangare na wannan sanarwar haɗin gwiwar ta Rice da Chertoff, "wannan canjin wata alama ce ta irin ƙoƙarin da muke yi, don tabbatar da ganin kare lafiyar jama'a da baƙi, saboda kare kan iyakokinmu, yayin da muke takatsatsan don tabbatar da ganin cewa mun buɗe ƙofofin karɓar baƙi da ɗalibai ko kuma waɗanda za su gudanar da harkokin ciniki a Amirka." ■

# Taron Shekara Na Shida Na Tsofaffin Ɗaliban Shirin Fulbright A Nijeriya Ya Tattauna Hanyoyin

## *"Inganta Harkokin Mulkin Dimokuraɗiyya Da Fahimtar Juna Da Ilimi"*

Daga
Susan Jatau da James Moolom
*Sashen Hulɗa Da Jama'a*
*Na Ofishin Jakadancin Amirka*

Don zama wani ɓangare na bukukuwan tsofaffin ɗaliban Shirin Fulbright a Nijeriya (FAAN), aka gudanar da Babban Taron Shekara na shida a Jami'ar Bayero da ke Kano (BUK), ranar 14 ga watan Fabrairu na 2006. Bukukuwan, waɗanda aka shirya domin inganta dangantakar da ke tsakanin tsofaffin ɗaliban na Shirin Fulbright da ci gaba da ɗaukaka burinsu na haɓaka shirin a Nijeriya, ya samu halarcin tsofaffin ɗaliban fiye da 50 da kuma tsofaffin ɗaliban jami'o'in Nijeriya 30. Manyan baƙi da dama, cikinsu kuwa har da Ambasada John Campbell da wakilin Gwamnan Jihar Kano, suka halarci bikin buɗe taron. Taron ya yi armashi ga manyan masana ilimi na Nijeriya, an kuma bayyana rawar da musayar ɗalibai ke takawa, wajen inganta abokantaka da fahimtar juna.

Lokacin da yake jawabi a wajen bikin buɗe taron, Jakandan Amirka a Nijeriya, Ambasada John Campbell ya bayyana cewa, ɗaya daga cikin muhimmancin wannan shirin na Fulbright shi ne "domin samar da ilimi, ko yaya, da nuna ƙauna ga juna, ko ya take, a harkokin duniya, wanda ke iya sa ƙasashe zama cikin lumana da abota da juna".



*Wakilin Gwamnan Jihar Kano kuma Kwamishinan Ma'aikatar Ilimi (a tsakiya) tare da Farfesa Shehu Galadanci (a hagu) da kuma Ambasada John Campbell (a dama).*



*Dokta Hussaina Abdullahi ta Jami'ar Usmanu Dan Fodiyo, a lokacin da take gabatar da lacca.*

Da yake magana game da taken taron, Ambasada Campbell ya ce "idan zumunci a tsakanin ƙasashe biyu ya ƙara danƙo, dangantakarmu ta yi faɗaɗar da za ta yi arangama da kalubalen da muke fuskanta a yau, da waɗanda muke hasashen za su abko mana.... to ba za mu taɓa rabuwa ba, amma za mu yi ƙoƙari da sababbin ƙungiyoyin siyasa duk

ko da matsalolin tattalin arziki da ke kunno kai kullum". Ya ce wannan ya haddasa wata sarƙaƙiya da dangantakar dole, tsakanin Nijeriya da Amirka.

Shugaban Kungiyar Tsofaffin Ɗaliban ta Nijeriya, Malam Abubakar Sokoto Mohammed, ya ce an tsara taken taron ne da nufin inganta fahimtar juna da haɓaka dangantakar da ke tsakanin Nijeriya da Amirka. Ya yi magana mai ƙarfi game da irin taimakon da Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka ke bai wa shirin na FAAN. Ya yi jawabi musamman a kan taimakon da ya sanya waɗansu wakilansu biyu suka halarci taron Ƙungiyar ta Fulbright a Baltimore. An kuma yaba wa abin da Nijeriya ta gabatar, wannan kuma shi ya yi sanadin da aka ba ta wakilcin Afirka, a Kwaƙƙwaran Kwamitin nan na Shirin Ayyukan Fulbright a Duniya (Global Fulbright Project).

Malam Abubakar Sokoto ya jaddada cewa, mafi yawan ƙasidun da aka gabatar a taron sun bincika batutuwa masu tsauri a Nijeriya, suka kuma shawarin da mafita, daga matsalolin. Ɗaya daga cikin irin wannan mafitar shi ne nazarin da Dokta Stella Williams ta Jami'ar Obafemi Awolowo da ke Ile-Ife ta yi, na samar da aiki ma ɗalibai 300 na jami'ar. Ta kuma bayar da shawarar a yi irin wannan shirin don sauran jami'o'in Nijeriya.

A cikin ƙasidar da ya gabatar, Farfesa Daniel Adene na Jami'ar Ibadan, wanda ya fara binciko ɓullar cutar masassarar tsuntsaye, watau cutar masassaran tsuntsaye, a Nijeriiya, ya bayyana irin alfanun da 'yan Nijeriya ke samu, na gina ƙasa, daga Shirin na Fulbright. An gabatar da ƙasidu da dama game da siyasa da al'adu da mulkin dimokuraɗiyya da tattalin arziki.

An kuma faɗaɗakar da waɗanda suka halarci taron a kan hanyoyin rubuta wa Shirin na Fulbright ƙwararan ƙasidu da kuma samun labarai a yanar-gizo.

Bugu da ƙari, Farfesa Chidi Ikonne na Jami'ar Fatakwal ya gabatar da wani Littafi na Uku da Kungiyar FAAN ta wallafa mai suna "Bayar Da Harkokin Tsaro da Dogaro da Kai". Littafin ya ƙunshi dukan ƙasidun taron Shirin Fulbright da kuma ƙwararan shawarwarin samun kayayyakin aikin nazari. ■

# Sashen Hulɗa Da Jama'a Ya Yi Tarurruka Da Musulmi A Kano

Abisa ga ƙoƙarin da yake yi na bayyana Amirka da fahimtarta ga ƙungiyoyin Musulmin Arewacin Nijeriya, Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka ya yi tattaki zuwa Kano, domin saduwa da matasa Musulmi, a wani fagen tattauna Tilasta Bin Dokoki a Tarayyar Amirka. An yi wannan taron ne a Jami'ar Bayero ta Kano, (BUK) ranar 17 ga watan Fabrairu na 2006.


*Shugabar Sashen Hulɗa da Jama'a, Misis Claudia E. Anyaso, tare da wakilan ƙungiyar mata Musulmi, a lokacin da ta miƙa masu kyautar komfuta domin inganta ayyukansu.*

Mataimakin Babban Jami'in Fannin Aiwatar da Doka na Amirka, Mista Robert Downey ne, ya gudanar da taron na tambayoyi da bayar da amsa, wanda aka shafe awa ɗaya da rabi ana yi. Mista Downey ya yi bayani game da harkokin tarayyar Amirka da kuma taimakon faɗaɗakar da jama'a game da tilasta bin doka ga Nijeriya. An kuma yi wannan taron ne, lokacin Babban Taron Shekara na Kungiyar Shirin Fulbright ta Nijeriya, a Kano. ■

# Matasa Ne Ginshiƙin Ci Gaban Kasa

## *-In Ji Ambasada Campbell*

### *A Lacca Da Ya Gabatar A Jami'ar Obafemi Awolowo Da Ke Ile-Ife*



Ambasada John Campbell

Manyan baƙi, maza da mata. A bisa al'ada, a nan ya kamata in ce da "sauran baƙi". Amman a san al'adar Yarbawa ce, muddin ba ka gaida mutum da kyau ba, to ba zai yi maka marhabin ba. Don haka "E ku Ile o".

Zan fara da miƙa godiyata da yabo ga Daraktan Cibiyar Zaman Lafiya na wannan Jami'ar. Ina kuma godiya da aka gayyace ni da in yi jawabi, a safiyar nan, in kuma nuna jin daɗina da irin nasarorin da wannan cibiya ta samu.

Ina sane cewa maƙasudin kafa wannan cibiyar shi ne don haɓaka harkokin matasa da ƙungiyoyinsu, wanda yana da kyau ƙwarai da gaske. Saboda haka ne ma na zaɓi in yi jawabi a kan "Matasa A Matsayin Ginshiƙin Ci Gaban Kasa".

Yawan Matasa na da muhimmaci a kowace ƙasa, musamman a ƙasashe masu tasowa, inda kashi 50 daga cikin 100 na yawansu, 'yan shekaru 18 ne da ƙasa da haka. A duk lokacin da matasa suka yi yawa a ƙasa, to irin alfanun da ƙasar za ta samu, ba ya misaltuwa. Asali ma, wani babban ɓangare a kasafin kuɗin ƙasa yana tafiya ne, wajen bayar da ilimi da harkokin kiwon lafiyar matasa. Babu wani arzikin da ya wuce na matasa a kowace ƙasa.

Wannan kuma shi ya kawo mu ga kalmar "ginshiƙi" da na yi amfani da ita a cikin jawabina. Burina, tun ina yaro, shi ne in nazarci harkokin gini, musamman tsofaffin gine-gine. A saboda haka ne ma, na yi ta yawo a ƙasashen duniya, domin gane wa idanuna gine-ginen tarihi. Ina kuma tabbatar maku cewa, ginshiƙi ya wuce a ce masa kwalliya a gini, shi ne tushen tsayiwar kowane gini. Don haka matasa su ne harsashi da ginshiƙin ci gaba da zaman lafiyar ƙasa. A waɗansu lokuttan ma, matasa ne ke biya wa ƙasa bukatun duk wani hanƙoro da fatarta.

Misali, a ƙasata, tarihi ya nuna cewa ɗaliban makarantun baƙaƙen fatar kudanci ne, suka fara zaman dirshan, lokacin boren 'yancin ɗan-Adam, a shekarun 1960, domin kawar da bambancin launin fatar da ake nuna masu. Ɗalibai ne kuma suka wayar da kawunan jama'a don kawo ƙarshen tsoma bakin da Amirka ta yi, a Yaƙin Vietnam, a shekarun 1970. A shekarun 1990 kuma, ƙoƙari da hanƙoron ɗaliban jami'o'i matasa ne, ya haifar da ci gaban na'urori masu ƙwaƙwalwar da aka samu canji ga fasahar harkokin gwamnati da na ciniki a duniya.

Matasan Afirka ma, sun bayar da gudunmawa ga ci gaban ƙasashensu. Matasan Afirka da suka yi karatu a ƙasashen waje ne, suka

zama kan gaba, wajen fafitikar neman 'yancin kai daga iyayen gijinsu. Su ne irin su Azikiwe da Nkrumah da Nyerere da su Senghor, waɗanda suka sama wa ƙasashensu mulkin kai.

Duk kuma tushen irin nasarorin da ɗaliban ke samu yana nan a jami'a. Ana iya tambayar "Mene ne a jami'a da yake tunzura ɗalibai ga ɗaukar waɗannan matakai?". Lokacin da yake yaba wa jami'o'in harshen Turanci, shekaru da dama da suka wuce, John Masefield ya ce, yana son jami'o'i ba don komai ba, sai don "wuri ne na waɗanda suka tsani jahilci, kuma suka amince cewa a daɗe ana yi sai gaskiya". Ma'ana shi ne waɗannan ɗaliban na samun ilimi a jami'a, su kuma yi amfani da shi, a duniyar da suke ciki. Suna lura da gaskiyar da ta wuce son zuciya, don haka suke kawo canji.

Wannan kuma shi ya sa a yau, ga Jami'ar Obafemi Awolowo da wannan ƙungiya, abin da kuka gani ya yi muku daidai?

Kafin ku gama tunanin wannan tambayar, bari in bayyana mu ku wata ƙididdiga. Ɗaya daga cikin muhimman ayyukan da gwamnatin ƙasata da Gwamnatin Tarayyar Nijeriya da kuma ƙungiyoyi masu zaman kansu, suka himmatu a kai, shi ne Shirin Shugaban Kasar Amirka A Kan Gaggauta Bayar da Tallafin Magance Cutar Kanjamau. Ba ku san cewa akwai aƙalla 'yan Nijeriya miliyan huɗu da ke ɗauke da ƙwayoyin cutar ƙanjamau ba? Wanda kashi ɗaya cikin goma na yawan jama'ar duniya ke nan da suke fama da cutar ƙanjamau. A lokacin da ta ziyarci ƙasar nan, a watan Janairu, Mrs. Laura Bush ta bayyana cewa Gwamnatin Amirka za ta keɓe dalar Amirka miliyan 163 a 2006, don taimaka wa Nijeriya yaƙar cutar ƙanjamau. Har yanzu kuma da sauran rina a kaba, kan yaƙi da annobar cutar ƙanjamau, a Nijeriya.

Wani al'amarin kiwon lafiya da Amirka da Nijeriya suka himmatu a kai ita ce cutar shan inna. A cikin 'yan shekarun nan, Majalisar Ɗinkin Duniya da gwamnatocin ƙasashe, ciki har da tawa, sun himmatu a kan kawar da cutar shan inna a duniya.

Nan da zuwa baɗi ma, a waɗansu ƙasashen sai labari. Jimillar waɗanda suka kamu da cutar a Nijeriya, a 2005, sun kai 763. Wannan jimillar ta kai kashi 41 cikin 100 na yawan masu cutar shan inna a duniya, kuma kashi 94 cikin 100 na cutar a Afirka. Dole ne a riɓanya irin ƙoƙarin da ake yi a Nijeriya, idan muna son shiga sahun ƙasashen duniya, don kawar da wannan mummunar cuta.

Wani abin sha'awa kuma da Amirka da Nijeriya ke haɗa ƙarfi a kansa, shi ne ilimin mata. Kididdiga ta nuna cewa idan mata suka ilmantu, to duk harkokin kiwon lafiya da na tattalin arzikin ƙasa, zai matuƙar bunƙasa.

Hukumar Kidaya ta Nijeriya ta bayar da rahoton cewa kashi 48 cikin 100 na mata ne ke da ilimi, a 2005, wanda ya nuna cewa akwai kashi 52 na matan Nijeriya da ba su yaƙi jahilci ba.

Bunƙasa ilimin mata wata tabbatattar hanya ce ta inganta ɓangarorin ci gaba, ina kuma jinjina wa gwamnatocin ƙananan hukumomi da jihohi da tarayyar Nijeriya, a kan ƙoƙarin da suke yi na magance wannan al'amari.

Kamar yadda kuka sani ne, cewa rashin aikin yi, musamman ga mata da maza waɗanda suka sauke karatu, ya kai abin da ya zama. To Shirin PRISMS, wani yunƙuri ne na Amirka, wajen samar da aikin yi a Nijeriya. Kasar Amirka ce ke gudanar da Shirin na PRISMS, tare da bankunan kasuwanci, wajen bayar da rance ga ƙanana da manyan ƙungiyoyin 'yan kasuwa. Wannan ma wata ƙalubale ce da ke bukatar a kula. Dole ne mu mayar da hankali ga rage yawan rashin aikin yi da talauci. Akwai sauran aiki a gabanmu. Duka kuma suna neman su tsone mana idanu. Amma idan muka daure, akwai karin maganar da ke cewa "Idan ka tarar da tsauni, hawansa shi ya fi maka, maimakon ka zauna a gindinsa ka rusa kuka".

A matsayinku na ɗaliban jami'a, kuna da dukan damar da kowa ke da ita a Nijeriya. Asali ma, iyayenku da malamanku da iyalanku da sauran jama'a sun zura maku idanu. Suna fatar ba kawai za ku amfanar da kawunanku ba ne, sai don a ci gajiyarku. Nijeriya na bukatar taimakonku a fannonin kiwon lafiya da ilimi da aikin yi da uwa uba, sauran harkokin ci gaban ƙasa.

Amma ba ina son in roƙe ku da ku bautar da kawunanku ne ga waɗansu ba. Ina ƙalubalantar ku ne zuwa ga samun biyan bukatar burinku na bayar da gudunmawa ga ci gaban Nijeriya. Wannan kuma shi ya kawo mu ga abin da muka zo yi a yau.

Idan ba ka son abin da ke tare da kai, me ya sa ba za ka canza shi ba? Wannan ita ce ƙalubalan da nake yi wa wakilan wannan taro. ■

# Musayar Dalibi Ya Zama Zakara A Wannan Watan

Abdulhafeez Lawal tsohon ɗalibi ne daga Nijeriya, a Shirin Musayar Ɗalibai Matasa (YES) na 2004-2005, wanda ya sha alwashin yi wa ƙasarsa hidima.

Kamar kowane tsohon ɗalibi, shirin ya ƙara wa Abdulhafeez basirar gaske. "Shirin ya ƙara mini ilimi da wayewar kai da kuma ɗa'a, kuma ya sanya na aminta da waɗansu al'amurran zamantakewar jama'a da suka bambanta da ni. Yanzu kuma na san cewa sanin bambanci na da kyau".

Lokacin da aka tambaye shi game da muhimmin abin da ya koya, a shirin musayar ɗaliban, Abdulhafeez ya kayar da baki ya ce, yana "koyar da mutum sanin yadda zai zauna da jinsin da ba nasa ba".

A gaskiya, ba samu wata gagarumar matsala ba, wajen sajewa da jama'a, a wajen shirin. Ya halarci Babbar Makarantar John F. Kennedy ne, da ke Cedar Rapids, ta yankin Iowa, inda ya nuna hazaƙa a fannin ilimi.

Bugu da ƙari, Abdulhafeez ya halarci tarurrukan ƙaro ilimi da dama, kamar Taron Sanin Makamar Shugabanci na Matasan Duniya a Des Moines da ke Iowa, don sanin cuɗanya da jama'ar duniya.

Ya shiga ayyukan sa-kai, ciki har da na Ranar Tunawa da Abinci ta Duniya, da shuka itatuwa da kafa gwangwalar zaman lafiya a Newton da ke Iowa, wadda ta nuna cewa "Zaman Lafiya, ya fi zama ɗan Sarki a Duniya", a cikin harsuna takwas.

Lokacin kuma da ya dawo Nijeriya, Abdulhafeez ya duƙufa ga yi wa jama'arsa hidima, a fannoni da dama.



Abdulhafeez Lawal



*Abdulhafeez Lawal a lokacin da yake wakiltar makarantarsa da ke Amirka a gasar guje-guje.*

A makarantarsu, shi ya zama na farko wajen kafa sabuwar Kungiyar Zaman Lafiya, wadda ya bayyana a matsayin wani "zauren yaɗa harkokin zaman lafiya, inda ake koyar da matasa ƙaunar tabbatar da zaman lafiya da sasanta rashin jituwa a tsakanin sa'o'insu".

Saboda zalaƙar da yake da ita, aka zaɓe shi da ya halarci wani taron kwanaki uku, na Zama Cikakken Ɗan Kasa na Duniya, da aka gudanar a yankin Niger-Delta da ke Nijeriya, a ƙarshen watan Nuwamba da farkon watan Disamba na 2005.

Lokacin wannan taron, yana cikin waɗanda suka gina ɗakin karatu na Oporoza, a Warrin Nijeriya da kuma halartar taron kawo zaman lafiya da kwanciyar hankali da bunƙasa shugabanci.

Bayan da ya dawo daga wannan taron ne, Abdulhafeez ya mayar da hankali ga Kungiyar Tsofaffin Ɗaliban Shirin YES don yin aiki da juna wajen bunƙasa yankuna. Wannan ƙoƙarin nasa ne, ya sanya ake girmama shi a Kungiyar ta YES, inda har aka zaɓe shi a matsayin Babban Sakataren Kungiyar ta YES da ke Nijeriya, a cikin watan Oktoba da ya wuce, lokacin da aka yi wani taron shekara a Kadunar Nijeriya.

A cikin watan Agustan 2005 kuma, Abdulhafeez tare da waɗansau ɗaliban Shirin YES huɗu, sun bayyana irin abubuwan da suka koya a Amirka, da kuma yadda shirin ya canja rayuwarsu.

Wata ƙungiya kuma mai suna Bunƙasa Zaman Lafiya da Ci Gaba, ta zaɓe shi a matsayin wakilin Hukumar Dattijai a watan Agustar 2005, saboda ƙwazonsa da gudunmawar da yake bayarwa wajen ci gaban ƙungiyoyi.

Haziƙancinsa na yin mu'amala da jama'a ta mutum da mutum da ta gidajen rediyo da telebijin ya sanya shi ya yi fice, a cikin tsofaffin ɗaliban da kuma jama'a. ■

# Amirka Ta Bayar da Kayayyakin Aiki Ga 'Yan Sanda

A wannan lokacin da duniya ke fama da laifukan ta'addanci da ƙarin tashe-tashen hankula, Jakadan Amirka John Campbell ya ce babban alfanu ne a samar wa rundunar 'yan sanda hanyoyin ƙwarewa da horo da kayayyakin aiki.

Ambasada Campbell yana jawabi ne, a wajen miƙa waɗansu kayayyakin aiki ga Rundunar 'Yan Sandan Nijeriya, a babban ofishinta da ke Abuja, ranar 1 ga watan Maris na 2006. Kayayyakin da aka bayar sun haɗa da amsa-kuwwa da takalma da ankwa da garkuwa da barkonon tsohuwa da sulke da waɗansu kayayyakin, masu dama, da 'yan sandan ke bukata don gudanar da



*Sufeto Janar na 'yan sandan Nijeriya, Mista Sunday Ehindero a lokacin da yake karɓar kayayyakin aiki da Ambasada John Campbell ya miƙa masa. A hannun dama, akwai Mista Robert Downey, Jami'in kula da fannin aiwatar da dokoki a Ofishin Jakadancin Amirka.*



*Ambasada John Campbell yana nuna ma Sufeto Janar Sunday Ehindero sauran kayayyakin aiki da Gwamnatin Amirka ta ba da su kyauta ga Gwamnatin Nijeriya.*



*Kayayyakin sun haɗa da silke da makarin harsashin bindiga da Ambasada Campbell ya yi ma Sufeto Janar Sunday Ehindero bayaninsu. Tare da su, akwai Misis Felia Edet ta Ofishin Jakadancin Amirka (a hagu).*

# Jawabin Mrs. Bush A Bikin Tunawa Da Ranar Mata Ta Duniya Na 2006



*Uwargida Laura Bush tare da Shugaban ƙasar Amirka, George Bush a lokacin da ta ke jawabin kan tunawa da Ranar Mata ta Duniya a fardar White House da ke Birnin Washington.*

Akowace shekara jama'ar duniya ke tunawa da Ranar Mata ta Duniya.

A bana ma, 2006, ina mai farin cikin saduwa da dubban mata daga ko'ina cikin duniya.

Na kuma yi imanin cewa, burin mata ne, a duk inda suke, su samu ilimi da zaman lumana da samun kula ta ɓangaren harkokin kiwon lafiya, su kuma kasaita, kazalika kuma a riƙa sauraren abin da za su ce.

Akwai sahihan alamomin samun ci gaban mata a dukan sassa na duniya, kuma ina mai alfahari da na auri mutumin da ke da ra'ayin inganta harkokin ci gaban jama'a. Amma, kada kawai a dogara da wannan kalami nawa.

Ku dubi irin yadda yake tafiyar da harkokin mulki, ta inda mata ke sadaukar da kai wajen bauta wa al'umma da kuma haƙurin da suke yi, a kowane matakin harkokin mulkin gwamnati.

Ku lura da Shirin Inganta Harkokin 'Yammata na Afirka. Muna godiya ga Kungiyar Bayar da Guraben Karo Ilimin 'Yammata ta Afirka.

Mata na amfana da gudunmawar ƙwayoyin magun-gunan warkar da cutar ƙanjamau, inda suke haihuwar jariran da suke kuɓuta daga kamuwa da ƙwayoyin cutar ƙanjamau, duk a sanadiyyar Shirin Shugaba Na Gaggauta Bayar da Taimako A Kan Cutar Kanjamau.

Yau 'yammata a Afghanistan na zuwa makaranta, yayin da matansu ke aikin gwamnati saboda irin taimakon da Amirka ke yi na kuɓutar da jama'ar ƙasar. A cikin makon da ya wuce ne, matar Shugaba Karzai ta faɗa mini a Birnin Kabul cewa, akwai yaran Afghanistan miliyan shida a makarantu, wanda kusan rabinsu 'yammata ne.

A wajen wannan bikin tunawa da matan duniya ne, da tarihinsu, muke girmama maza da matan da suka shahara a fannonin yin adalci da girmamawa da kuma bai wa mata damar da Allah ya ba su. ■

---

ayyukansu yadda ya kamata.

Babban Sufeton 'Yan Sandan, Sunday Ehindero ne ya karɓi kayayyakin da aka bayar, a madadin Gwamnatin Tarayyar Nijeriya.

Tun cikin 2002, Gwamnatin Amirka take bai wa Gwamnatin Nijeriya kayayyakin da suka kai na fiye da dalar Amirka miliyan biyu, don hana cin hanci da rashawa da hana fataucin bil-Adama da ƙwayoyi da inganta harkokin 'yan sanda, su kasance na zamani, da kare rayuka da dukiyar al'umma kazalika da almundahanar kuɗi. ■

Zuwa ga Edita,
Bayan gaisuwa mai yawa da fatan alheri, bayan haka na rubuto wannan takardar ne domin sada zumunta.
Bayan haka, ni ɗalibi ne, amma ina neman cikakken bayani a kan Shirin Tallafa wa Ilimi na Amirka.
Daga ƙarshe ina son a aiko mini da MAGAMA. Na gode sai na ji daga gare ka.
Ni ne Naka,
Ya'u Bala,
Bakin Kasuwa, Gusau,
Jihar Zamfara.

Zuwa ga Edita,
Ina yi maku murna da buɗe wannan sashen na Hausa.
Don Allah ina roƙon ku da ku ƙirƙiro wani ɓangare da za ku riƙa bayar da rahotannin da suka shafi kimiyya, domin za a ƙaru da ku ta wannan fannin, musamman kamar abin da ya shafi sararin samaniya.
Na biyu, ina roƙon a rinƙa aiko mini da dukan kofin da kuka buga daga lokacin da kuka sami wannan wasiƙar.
Wassalam,
Naku,
Umar Yusuf
Anguwar Juma,
Zaria.

Zuwa ga Edita,
Bayan gaisuwa mai yawa tare da fatan alheri gare ku baki ɗaya, watau da kai da ma'aikatanka, bayan haka ina so in nuna ra'ayina game da wannan mujallar taku mai matuƙar gamsarwa da kuma ilmantarwa dangane da wayar wa da mutanen karkara kai dangane da ayyuka na alheri.
Haka kuma ita wannan mujallar tana nuna dangantaka ta ƙasa da ƙasa da fatan Allah Ubangijin Sarki, Allah Maɗaukaki ya ƙara taimakon ku kuma ya yi maku jagora, amin.
Ni ne Naka,
Mohammed Inuwa Adamu Zakirai,
Zakirai K/Fada,
Gabasawa Local Government,
Kano.

Zuwa ga Edita,
Gaisuwa mai yawa tare da fatan alheri. Yaya ayyukan yau da kullum? Da fatan komai yana tafiya daidai.
Ina mai sanar da kai cewa na samu mujallarku ta watan Nuwamba 2005, lokacin da na je Ɗakin Karatu na Murtala Mohammed da ke Kano, na kuma karanta abubuwa masu ƙayatarwa da kuma ƙaruwa.
Ina kuma fatan za ku ci gaba da aiko mini da duk wata mujallar da za ku buga nan gaba, da fatan bukatata za ta samu karɓuwa.
Ni ne Naka,
Yusuf Abubakar Garba,
Fagge,
Kano.

***Kuma zaku iya karanta mujallarmu a intanet. Don haka, ku aiko mana da adireshi ku na e-mail a wannan adireshi:*** magama-ng@lists.state.gov ***domin mu rika aiko muku da mujallarmu kai tsaye a duk lokacin da muka fito.***

## RA'AYINKA

Idan ka samu mujallar *Magama,* muna bukatar ra'ayinka game da ita.
Suna ..................................................
...........................................................
Adireshi na e-mail..............................
...........................................................
...........................................................

Za'a iya aiko mana da wasiƙu ta hanyar e-mail a wannan adireshi: magama@state.gov

*Ka aiko mana da dukan bayanai ta hanyar e-mail ko kuma akwatin gidan waya mai lamba: 5760 Garki, Abuja.*

e-mail zuwa ga edita: magama@state.gov

# Taron Kungiyar Tsofaffin Daliban Shirin Musayar Ɗalibai Da Malamai “Fulbright” Ta Nijeriya (FAAN) A Kano



Dokta Aminigo na Jami’ar Fatakwal a lokacin da take gabatar da lacca a kan hanyoyin ciyar da ƙasar Nijeriya gaba.



Malam Abubakar Sokoto Mohammed, shugaban wannan ƙungiya (na uku daga hagu) a lokacin da yake zantawa da Ambasada John Campbell (na biyu a dama) da kuma Misis Shirley Lisenby, jami’ar Sashen Al’adu na ofishin Jakadancin Amirka (a dama).



Farfesa Chidi Ikonne a lokacinda yake gabatar da littafin ƙungiyar tsofaffin ɗaliban shirin musayar ɗalibai da malamai “Fulbright”.




Littafin ƙungiyar



Daga hagu: Ba’amirke ɗan asalin Nijeriya da ke koyarwa a Jami’ar Abuja, Farfesa Emeka Okoli, da Mista James Moolom, Jami’in Sashen Al’adu na ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja, sai kuma mista Henry Mendelsohn, Jami’in kula da Ɗakunan karatu na Amirka tare da sauran manyan ƙwararru da suka hailarci taron.



Misis Claudia Anyaso, Shugabar Sashen Hulɗa da Jama’a (a dama) tare da takwararta ta ƙaramin Ofishin Jakadancin Amirka da ke Legas, Misis Atim Eneida Georg da kuma ɗaya daga cikin manyan malamai da suka gabater da ƙasidu a wannan taro.



Wakilin Gwamnan Jihar Kano kuma kwamishinan Harkokin Ilimi (a tsakiya) tare da Ambasada John Campbell ( a dama) da kuma Farfesa Shehu Galadanci (a hagu)



Ɓangaren ɗalibai da malamai da suka hailarci wannan taro.

22 Ga Watan Afrilu Ce Ranan Bikin Kare Muhalli, Amma Ya Fi Kyautatuwa Mu Kare Muhallinmu A Kullum. Amintaccen Muyhalli Mai Ɗorewa Shi Zai Kawo Mana Kyakkyawar Rayuwa.



# Afrilu 2006

| Sun | Mon | Tue | Wed | Thu | Fri | Sat |
|---|---|---|---|---|---|---|
| 30 | 31 | Bayanin da Sashen Hulda da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Ikko. | | Bayanin da Sashen Hulda da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Abuja. | | 1 |
| 2 | 3 | 4 Bayanin da Sashen Hulda da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Ikko. | 5 | 6 Bayanin da Sashen Hulda da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Abuja. | 7 | 8 |
| 9 | 10 | 11 Bayanin da Sashen Hulda da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Ikko. | 12 | 13 Bayanin da Sashen Hulda da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Abuja. | 14 | 15 |
| 16 | 17 | 18 Bayanin da Sashen Hulda da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Ikko. | 19 | 20 Bayanin da Sashen Hulda da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Abuja. | 21 | 22 12 Ga Watan Afrilu Ce Ranan Bikin Kare Muhalli. |
| 23 | 24 | 25 Bayanin da Sashen Hulda da Jama'a ke yi wa taron 'yan jaridu a Ikko. | 26 | 27 | 28 | 29 |